

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Ɗandana Amincewarsa

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Don samun tanadin Allah domin ƙiyayya, dole ne ka fahimci muhimman abubuwa guda biyu. Na farko, Allah bai yi tanaji da yawa dabam dabam ga kowace buƙatar ɗan adam ba. Maimakon haka, ya yi guda ɗaya ne kawai, tanadin da ya ƙunshi dukan buƙatun mutane. Wannan ya ƙunshi tanadin gaba ɗaya wanda shi ne mutuwar Yesu ta hadaya a kan gicciye.

Na biyu, abin da ya faru a kan gicciye musaya ce da Allah kan Sa ya shirya. Duk mummunan sakamakon zunubanmu sun hau kan Yesu saboda, ta haka a maido da dukan abubuwan amfana na biyayyar Yesu marar zunubi ta zama isasshiya a gare mu. A namu ɓangaren, babu abin da muka yi da ya sa muka cancanci wannan, kuma ba mu da wata cancanta ko haƙƙin cewa namu ne. Wannan ya samu ne kawai ta wurin ƙaunar Allah marar misaltuwa.

Saboda haka, ba shi da amfani mu fuskanci Allah da wani tunanin cancanta ko ta ikirarin cewa muna da shi. Babu abin da za mu bayar na kanmu da za a iya kwatanta shi da cancantar hadayar da Yesu ya miƙa a madadin mu.

Kristi ya ɗauki ƙiyayyar mu a kan gicciye, tare da dukan kunya da cin amana, azaba da baƙin ciki. A gaskiya ma, karyayyiyar zuciya ce ma ta zama dalilin mutuwarsa. Mun sami karɓuwa saboda ƙiyayyar da ya sha. Mun sami karɓuwa a cikin Kaunataccen. Musaya ce. Yesu ya ɗauki muguntar domin mu sami alherin. Ya ɗauki baƙin cikinmu domin mu sami farin cikin Sa. An buɗe hanya domin mutum ya je wurin Allah ba tare da kunya ba, ba tare da laifi ba, ba tare da tsoro ba. Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami amincewar Sa.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta tabbacin musayar da Yesu ya yi mani: An karɓe ni saboda ƙiyayyar da ya sha. Na karɓi alheri saboda Ya ɗauki muguntar. Ina da farin cikin Sa domin Ya ɗauki baƙin ciki na. Ina furta cewa Yesu ya ɗauki ƙiyayya ta domin in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-144-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.